Made for minds.

# Da’ar aiki

Darajarmu. Dabi’armu. Halayyarmu.

# Rayuwa da dabi'un mu



Zuwa ga abokan aiki,

DW (Deutsche Welle) na isa ga mutane da yawa a faɗin duniya fiye da kowane lokaci a baya, wanda ya sanya ta samu babban daukaka da girmamawa a matsayinta na murya mai zaman kanta. Muna so mu fadakar da jama'a — musamman inda ake tauye musu damar samun bayanai da kuma farfaganda da sannan babu damar bayanai mabambanta. A nan ne mu kuma baiyana sabanin matsayi.



**Muna haɓaka damar samun bayanai ba tare da shamaki ba da kuma 'yancin faɗin albarkacin baki a duk faɗin duniya.**

Dukkanin mu a DW muna da manufa guda: ra'ayin 'yanci, riko da kare 'yancin ɗan adam, dimukuraɗiyya zuciya daya, haƙuri da juna da kuma nuna gaskiya ga jama'a. Wannan shi ne ya sa muka yi watsi da dukkan nau'in nuna bambanci da suka hada da jima'i da wariyar launin fata da kuma kyamar Yahudawa. Hakkin da ya rataya a wuyan Jamus na tarihi game da kisan gillar da aka yi wa Yahudawa shi ma dalili ne da muke goyon bayan 'yancin Isra'ila na wanzuwa. Mun jajirce a kan wadannan kudirori. Ana iya ganin wannan a zahiri ba ma kadai a shirye-shiryen da muke gabatarwa a aikinmu na jarida ba da kuma aikace-aikacen bunƙasa manufa ta cibiyar horon 'yan Jarida DW Akademie da kuma shiryen-shiryen ilimi, har ma a cikin cuɗanyarmu ta yau-da-kullum na mutane daga ƙasashe fiye da 160 a lamuransu daban-daban.

A matsayinmu na kamfanin watsa labarai a faɗin duniya wanda kuma ke da sahalewa ta jama'a, muna da wani nauyi da za mu sauke ga masu amfani da kafofinmu, ayyuka, saye da sayarwa da kuma abokan huldar kasuwanci, al'umma da kuma muhalli. Wadannan ka'idojin aiki suna kwatanta yadda muka fahimci wannan nauyi a ciki da waje.

Muna aiwatar da waɗannan manufofi da ƙa'idoji, halayya da nagarta da muke isarwa kuma muke tallatawa a faɗin duniya da DW ita kanta tare da haɗin gwiwa da abokan huldarmu. An bayyana wannan a ka'idojin da'ar aikinmu.

A matsayin ka'idar da'ar aiki, ya yi bayani taƙaitacce na tsarin halayya da dabi'u da suke yi mana jagora a ayyukanmu na yau da kullum da kuma hulda da juna. Yin biyayya ga doka yana da muhimmanci a

gare mu a dukkan abin da muke yi. A saboda haka dokokin tsarin aikin suna tabbatar da cewa mu gudanar da dukkan ayyukanmu kan tafarkin doka, wanda dukkan ma'akatan DW za su bi karkashin tsarin doka yadda ta fuskar da'a ba za a iya sukar ayyukanmu ba.

Karin wasu ƙa'idojin su ne Ɗa'ar Shugabanci na DW, waɗanda yanzu aka aiwatar a duk faɗin kamfanin. Dokokin tsarin aikin suna da muhimmanci wurin tabbatar da mutucinmu da nasararmu, a nan Jamus da kuma duniya baki daya. Manufar ita ce zaburar da duk waɗanda suke aiki domin tabbatar da burinmu a DW zuwa muhimmancin waɗannan ƙa'idoji da dokoki da muke da su na cikin gida da kuma muhimmancin biyayya gare su. Dokokin tsarin aiki tilas ne a kan dukkan ma'aikatan Deutsche Welle da kuma rassanta.

Za mu binciki saɓawa dokokin tsarin aiki mu ɗauki duk matakin da ya dace musamman wadanda suka shafi dokokin aiki. A matsayin kafa mai watsa labarai wadda ke goyon bayan 'yancin faɗin albarkacin baki da kuma ra'ayi a duk faɗin duniya, muna samar da wani yanayi a cikin DW wanda ya amince da bambancin fahimta mai ma'ana.

Na ku,
**Peter Limbourg**
Babban Darakta

“Mu duka mun yi tarayya kan manufa daya.

# Kundin da’ar aiki

Kundin da’ar aiki ya shafi dukkan dokoki da yarjeniyoyi da aka cimma bisa manufa da kuma ka’idojin cikin gida na DW da suka danganci DW musamman wadanda suke kunshe a littafin jagora na DW. Hakika wadannan dokoki na da’a za su ci gaba da zama masu amfani a karkashin kundin da’ar aiki.

A matsayin ma’aikata, ana bukatar mu fahimci wadannan dokoki. Tambayoyi a kan daidaikun dokoki da ka’idoji za a iya gabatar da su ga manajoji da jami’an tabbatar da bin ka’idoji da kuma bangarorin da abin ya shafa.

# Abin da ya bambanta mu da saura

**Kimarmu –**
**labarai ba tare da son zuciya ba**

Manufarmu: A matsayin kafa da ba ta nuna son zuciya, kafar yada labaran Jamus, muna bayar da labarai da bayanai ga jama'a a duniya baki daya, tare da ba su 'yanci su baiyana ra'ayinsu.

Mun kasance har zuci *(Made for Minds)* A zantawa da masu amfani da shafukanmu da kuma tashoshi abokan huldarmu, muna sadar da sabon hange wanda ya dogara da majiya mai tushe domin zukata da tunani na kaifin basira a duk faɗin duniya. A lokaci guda, muna bawa mutane dama kyauta ga kayayyakin koyo. Muna taimaka masu tsara ra'ayoyinsu cikin 'yanci ba tare da katsalandan ba, kuma su baiyana su cikin 'yanci babu shamaki, ta yadda za a samar da al'umma da za ta zauna kan tafarkin gaskiya da wanzuwar dimukuraɗiyya tare.

Waɗannan su ne burorinmu, amma yadda muke tunkarar su, shi ma yana da muhimmanci: muna da ɗabi'u bayyanannu waɗanda ra'ayinmu ya zo daya a kansu da abubuwa bayyanannu da muke tsammani ga kawunanmu da kuma hanyar da muke hulɗa da juna. Suna tafiya ne tamkar zare da ke gudana a aikace-aikacenmu suna kuma tabbatar da ra'ayinmu da ɗabi'armu ta yau da kullum.

### Kudiri zuwa ga ʼyanci

ʼYanci, dimukuraɗiyya da kuma ʼyancin ɗan adam su ne ginshikin aikinmu na jarida da raya cigaba da kuma wanzuwar siffa da cikar kamalarmu. Muna ƙaunar ɗabiʼun ʼyanci kuma a duk inda muke muna daukar matsaya ta rashin nuna bambanci musamman a kan dukkan nauʼin nuna wariya da suka hada da jimaʼi da wariyar launin fata da kyamar Yahudawa. A saboda tarihin Jamus, muna da hakki na musamman ga Israʼila.

### Tattaunawa ta zahiri, da kawance a duk faɗin duniya

Rayuwar mutane ta zahiri da kuma bukatunsu su ne ruhin ayyukanmu a jerin aikace-aikacenmu na jarida da na DW Akademie. Tsage gaskiya komai dacinta, da kawance a sassan duniya da larduna, muna tattaunawa da jamaʼa a duk faɗin duniya. Jerin shirye-shiryenmu da aikace-aikacenmu suna bayyana sabuwar mahanga a kowane lokaci da kuma duk inda ake bukata. Muna haɓaka musaya mai inganci kuma muna ɗaukar duk mutane da girmamawa — a ko da yaushe kuma a koʼina.

### Kaifin basira da mahanga mabambanta

Bambance bambancenmu da kuma ƙwarewarmu su ne manyan jarinmu. Muna kallon duniya tare da tunani mai zurfi, muna ɗaukar sabbin hanyoyi tare da ƙwarin gwiwa, mu yi tambayoyi masu tsauri sannan mu samar da amsoshi masu ʼyanci kuma masu makama. Sassanmu masu harsuna dabam-dabam, a cikin kasashe fiye da 60 a duk faɗin duniya, tare da masu amfani da shafukanmu da abokan huldarmu, muna samar da shirye-shirye masu kayatarwa da matuƙar inganci da kuma maʼana. Muna inganta haɓaka tsarin kafar sadarwa mai ʼyanci, bayar da damar samun bayanai, da kuma shata mizani abin koyi domin ilimi mai nagarta da kuma aikin jarida mai zaman kansa. Muna musayar raʼayoyi muna kuma kyakkyawar amfani da bambance-bambancenmu domin ingantacciyar nasara da fahimtar juna.

Waɗannan ɗabiʼu sune ginshiƙin dokokinmu na daʼar aiki — tabbatar da haɗin kai mai amfani da kuma girmamawa.

> “Muna musayar raʼayoyi da amfani da bambancinmu don samun nasarar juna.

# Biyayyar mu ga doka da ƙa'idoji

Tare da ka'idojinsa ga dabi'a, Da'ar Aiki ta kunshi mu'amala tsakanin DW da kuma fayyace tsarin aikinmu na yau da kullum, da kuma bangarori na aikin jarida. Tabbas, dokokin da suka dace da takamaiman ka'idojin kamfani na ci gaba da aiki a karkashin ka'idojin Da'ar Aiki.

Hukumar gudanarwa da shugabanni na zama abin koyi saboda haka alhaki ya rataya a wuyansu na ba da gudunmawar ganin an yi aiki da Da'ar Aiki.

DW na sa rai ma'aikatanta su ba da kulawa ta musamman ga wadannan batutuwa. Keta su na iya zama laifi karkashin dokar kwadago.

## Hana wariya karkashin "Dokar Ba da 'yanci daidai wa daida" wato (Allgemeines Gleichbehandlungsgesetz (AGG))

Ba za a lamunta da kowane irin nau'i na nuna wariya, ko na jinsi, ko launin fata ko kyamar Yahudanci karkashin dokar AGG ba. Ba za mu juya baya ga duk wani ma'aikaci, abokan tarayya ko wasu ɓangarori waɗanda muke hulɗa tare da su a cikin ayyukanmu ba ko dai a kan nuna kyamar Yahudanci ko wariyar launin fata ko bisa dalilan kabilanci, jinsi, addini ko ra'ayi dangane da lamuran duniya, nakasa, shekaru ko jinsi da mutum ya zaba wa

kansa ba. Muna ƙin cin zarafi da cin zarafi na jima'i. Haka nan an haramta yada zagi da yi wa wani bangare na al'umma kazafi.

Ba za mu lamunci tsokana ta ƙabilanci ko nuna ƙyamar launin fata ko haramtacciyar halayya

### Iyaka na 'yancin fadin albarkacin baki

kamar karyata aukuwar kisan kare dangi na Holocaust ba.
Muna sane da cewa 'yancin fadin albarkacin baki yana ƙarewa loka-cin da ya ketare layi zuwa cin zarafi, lalata a hanyar da ba ta dace ba da duk wata ɗabi'a ta batanci kamar yada karerayi, batanci ko zagi.

Mun kuma san cewa 'yancin faɗar albarkacin baki bai shafi karyata aukuwar Holocaust ko wani ra'ayi sabanin yadda ake kallonsa ba.

> **Ba za a yarda da nuna bambanci ba, ko a cikin mu'amalarmu da juna, ko a cikin aikinmu.**

A matsayinmu na ma'aikatan DW, wajibi ne mu yi taka-tsantsan dangane da abubuwan da a kan wallafa a kafafan sada zumunta da sauran wallafe-wallafe na wajen aiki ko na radin kai ba. Wannan hani ya samo asali ne saboda nauyin da ya rataya a wuyanmu ga kimar DW da kuma nauyin da ya rataya a wuyanmu ga DW a mat-sayin mai daukar aiki da sauran ma'aikata kamar yadda aka tanada a cikin kwantaragin aikinmu. Bisa la'akari da matsayinmu da fannin ayyukanmu, wajibi ne mu tabbatar da cewa halayenmu a bainar jama'a sun dauki wani tsari wanda hakan ba zai yi illa ga sahihan muradun DW ba. A ko da yaushe za mu kauce da kuma nesanta kanmu daga yin wasu abubuwa da furuta kalaman nuna wariyar jinsi, ko launin fata ko kyamar Yahudanci. Irin waɗannan maganganun na iya haifar da saka-mako dangane da dokar kwadago ciki har da sallamar ma'aikaci.

A matsayinmu na ma'aikata, mun sani kuma muna bin muhim-man dokoki, daukacin yarje-jeniyoyi umarni na DW na cikin gida, musamman, ƙa'idoji da aka bayyana a Karamin littafi na DW waɗanda suka dace da ayyukan-mu. Waɗannan ƙa'idoji sun ci gaba da aiki kuma babu wata hanya da suka ci karo da Tsarin da'ar gudanar da aiki.

# Hanyoyinmu na mu’amala da juna

### Girmamawa

Muna aiki tare ta hanyar gaskiya da kuma girmamawa.
Muna girmama kowane mutum ba tare da la’akari da ƙabila, jinsi, addini ko naƙasa, shekaru ko yanayin mu’amalar jinsi ba.
Muna daraja bambancin ra’ayi.
Mun tsare manufar "ba-sani-ba-sabo " dangane da cin zarafi ta fuskar jinsi a wurin aiki.
Ba za mu lamunci tozarta muƙami ko ta wace irin fuska ba.

### Nuna gaskiya da haɗin kai

Muna musayar bayanai a bayyane kuma a kan lokaci.
Muna hada kai a wurare da dama na harkoki da kuma sassa.
A shirye muke mu karbi sabbin ra’ayoyi da kuma ƙirƙira. Girmamawa, babu rufa-rufa, da haɗin kai, amana, biyayya, da al’adar karbar suka ko bayani mai ma’ana da kuma shugabanci da halayyar aiki da suka dace da ka’idojin da’ar aiki da muka amince da su, su ne ginshiƙin aikinmu.

### Amana

Kofarmu a bude take kuma a zahiri.
Mun kasance abin dogaro tare da jajircewa a kan aiki.
Mun samar da yanayin aiki wanda ke bayar da damar sadarwa da suka mai ma’ana.

> “Komai a fayyace da inganci.

## Ɗabi'ar suka mai ma'ana

Mun samar da yanayi na yin suka mai ma'ana tare da nazarin matakan da ake bi a yanzu domin samar da sabbin hanyoyi ta hanyar yin waiwaye a kan dabi'unmu.
Muna karbar kuskure a matsayin dama ta yin gyara.
Mun tabbata cewa mutane na iya canzawa su kuma canza tunani da ra'ayoyinsu.
Muna kokari wajen magance rashin jituwa.
Ba mu yada wani rashin gaskiya game da wakilan DW, manajoji da ma'aikatanta.

## Biyayya

Mun riƙe ɗabi'a da matakan cimma nasarar kudirorin DW.
Mun kara azama wajen fasalta hanyoyin kawo sauyi.
Mun jajirce wajen kare gaskiya da martaba.

## Aiki da daidaitacciyar manufa

Muna aiki cikin 'yanci domin cimma manufar DW.
Muna amfani da sabbin hikimomi don ƙarfafawa da ƙwarin gwiwar ƙirƙira.
Muna ƙoƙarin cimma manufa.



# Mua'amala da abokan hulɗarmu da kuma wasu daban

### Hakkin mallaka

Muna girmamawa kuma muna kare hakkin mallakar kirkira na wasu kamar yadda dokoki da suka dace suka tanadar.

### Saɓani a kan wata bukata

Muna yanke shawara kan harkokinmu daidai da muradun DW. Ba ma bari bukatun wasu ko dangantaka ta daban su yi tasiri a kanmu.

Mun jajirce wurin bayyana abubuwan da mai yiwuwa za su iya kawo saɓani a kan wasu muradu.

Muna tabbatar da cewa harkokinmu da kuma abokan huldarmu ba su sami saɓani a kan wata bukata ba.

### Cin hanci da yin alfarma

Muna adawa da cin hanci ta kowace fuska kuma muna kaucewa kowace irin siga ta cin hanci.

Muna kaucewa kowace irin alfarma, cin hanci ko wata hanya ta kyauta ga wani.

### Abokan hulda

Muna amfani da sanarwar DW wajen zaban abokan hulda.

## “Muna daukar matakai na aiki bisa muradun DW.

### Kyautuka da wasu fa’idoji

Muna ƙin amincewa da kyautuka, gayyata da ragin kuɗi (ga ’yan jarida) wanda zai jawo shakku ga ’yancinmu kuma ya iya jawo mu kasa ko rashin yanke wata shawara dangane da harkokinmu.

Muna karbar wasu kyautuka, gayyata da fa’idoji ne kawai idan an nuna gaskiya kuma an bi dukkan dokokin da suka dace da kuma ƙa’idoji na cikin gida.

Muna bayar da kyautuka da gayyata ’yan takaitattu ne kawai. Batun mai ya fi dacewa ya dogara ne ga abin da Jamus ta ga ya dace, a gefe guda kuma da yin la’akari da ƙasar da ake so a baiwa.

### Samarwa da isarwa

Muna samun kayayyaki, aikace-aikace da kuma shirye-shirye a kan tushen inganci, tattalin arziki da gogayya kamar yadda dokoki suka tabbatar da kuma ƙa’idoji na cikin gida. Hukuncin saye ya dogara ne a kan tantance ingancin kaya da ayyuka na mai samarwa. Yarjejeniyoyi waɗanda suka saba da sharuddan gogayya ba za a amince da su ba.

# Ɗaukar da muke yi wa bayanai

## Adana Sirri

Muna ɗaukar sirrin kasuwanci da sirranta bayanai da kulawar da ta dace. Wannan ya hada da bayanai da suka shafi labarai da muke bayarwa da kuma wasu bayanan da ba su dace a bayyana su ba.

Muna bayar da damar samun bayanan sirri ne kadai, ko da kuwa ta cikin kwamfuta ne ga ma'aikatan da suke bukatarsu kawai.



## Kariyar bayanai

- Muna tattara bayanan da suka dace ne kawai (tsimin bayani).
- Muna tabbatar da sirri wajen tattara bayanan da doka ta amince da su, amfani da kuma sarrafa bayanai na wani da kuma kare bayanan daga amfani da su ta hanyar da ba ta dace ba.
- Idan za a yanke shawara kan adana bayanai ko sauya fasalin ajiyarsa, muna girmama sirrinsa.


## IT da tsaron bayanai

- Yayin aiki da tsare-tsaren IT, wato bayanai ta kwamfuta muna lura da dokoki da kuma ƙa'idoji na IT da kuma tsaron bayanai domin kare yin amfani wanda bai dace ba na wadannan tsare-tsare, a cikin gida da kuma waje.
- Muna sane da barazana ga tsaron bayanai na DW wanda ka iya tasowa daga rashin kulawa wurin amfani da tsare-tsaren IT mu kuma yi abin da ya dace.



> “Muna taka-tsantsan wajen aiki da bayanai.

# Huldarmu tare da jama'a




> **“Muna bayyanawa a fili ko muna aiki a matsayin masu zaman kansu ko a matsayin ma’aikatan DW.**

Mu da kanmu ba ma amsa tambayoyi daga ’yan jarida da kuma kamfanonin yada labaru dangane da DW a dunkule, amma muna mika wannan ga sashin Sadarwa na Gamayya, wanda yake tsarawa da kuma bayar da bayanan.

A dukkan sadarwa, muna fayyacewa ko muna yi ne a matsayin radin kanmu ko kuma muna yi ne a matsayin ma’aikatan DW.

Domin kaucewa yiwuwar sabani na son zuciya, muna shiga ayyuka na waje ne kawai wadanda za su iya yin tasiri wajen haskaka bayanai ga jama’a bisa tsari da amincewar dokokinmu na cikin gida.

# Tsaronmu da kuma tsari mai ɗorewa




“Muna aiki
kan tafarki
mai dorewa.

Muna bin ka'idoji da dokokin kiyaye lafiya don kaucewa haddura yayin gudanar da aiki.

Muna bin dokokinmu wajen tura ma'aikata wuraren da ake rikici.

Muna aiki cikin da'a musamman wajen alkinta albarkatun kasa da muhalli ta yadda za a sabunta amfani da albarkatun don cin moriyarsu.

Muna tabbatar da cewa ayyukan ba sa haifar da wata illa ga abokan huldarmu (babu cutarwa).




# Yadda za mu kula da kayan kamfani

Muna amfani da kayan aikinmu da kuma sauran kayayyaki na DW da kulawar da ta kamata.

Muna bayar da sakamakon aikinmu ga DW.

Muna kula da ƙa'idojin aiki da kuma tattali wurin amfani da kayan aiki.



“Muna kula da inganci da tattalin arziki.


Made for minds.

# Ka’idojinmu na edita da kuma nagarta

Muna sane da nauyin da yake kanmu na al’umma a matsayinmu na masu tasiri kan ra’ayin al’umma saboda haka muna kiyayewa.

Muna gudanar da aikinmu kamar yadda dokar DW ta tanada da kuma tsarin Da’ar aiki.

Muna aiki kan tafarkin ka’idar aikin jarida ba tare da katsalandan ba kuma ba tare da tasiri daga abin da wasu daban ke so ba.

Muna girmama bambancin ra’ayi dangane da mafi rinjayen al’umma da ra’ayoyinsu mababbanta da kuma inganta tattaunawa.

Muna lura da yin taka tsan-tsan wurin aikin jarida, gudanarwa ta hanyar bincike sannan mu bayar da rahoto da daidaitaccen bayani.

Muna lura da dokoki da suka danganci rabewa tsakanin talla da bayanai da suka shafi labari.

Muna kula wajen kare sirrin al’umma da cikakkiyar nutsuwa wajen aiwatar da bayanai da ra’ayoyi da kuma hotuna.

Muna daraja dokokin gudanar da shafukan sada zumunta na DW da kuma dokokin tsarin aikin jarida na shugabar Editoci.



“Muna bin ka’idojin aikin jarida.



# Ka’idojin aiwatar da dokokin tsarin aiki

## Hukuncin karya dokokin DW na da'ar aiki

Idan ya kasance an karya dokokin da'ar aiki, DW za ta dauki matakai domin fayyacewa da kuma kare aukuwar duk wani abu maka-mancin hakan a gaba. Da farko wadannan matakai za su kasance na tattaunawa da ma'aikacin da abin ya shafa domin baiyana masa muhimmancin kundin da'ar aiki tare da manufar kawo sauyi ga halayyar wannan mutum ga dokar da aka saba. Girman laifin da aka aikata shi ne zai fayyace wadanne matakai ne na dokar kwadago da suka dace a dauka. Idan ma ya zama wajibi wadannan suna iya hadawa da korar ma'aikaci ko kuma yanke hulda da shi.

## Waɗannan tambayoyi na iya taimaka maka bin dokokin tsarin aiki

- Shin ina bin ƙa'idojin shari'a da dokokin kamfani waɗanda suka dace?
- Shin na tuntubi sauran bangarori da ke da ruwa da tsaki a kan lokaci don yanke hukunci?
- Shin na yanke hukuncin ne kawai kan muradun DW ba tare da son zuciyata ba?
- Mene ne tasirin hukuncina a zahiri? Shin hukuncin zai iya zamantowa abin dubawa daga wasu daban? Shin kimar DW za ta ɗore?
- Shin zan iya sulhunta shawarata da tunanina?

Idan za ka amsa dukkan tambayoyin da cewa “Eh”, to hukuncinka za ta yi daidai da da'ar aiki.  Amma idan ba ka tabbatar ba, wadannan mutanen za su iya taimaka maka.

# Mutanenmu da za a tuntuɓa idan ana da tambaya



**Idan ba ka tabbatar ba ko kana da wata tambaya dangane da bin dokokin tsarin aiki, daure ka tuntuɓi babban jami'in gudanarwa na sashinka ko Jami'i mai lura da aiwatarwa.**



## Mutanenmu da za a tuntuɓa idan aka karya doka

Dokokin tsarin aikin tilas ne a kan dukkan ma'aikatan DW.

Idan ka lura da yiwuwar ana keta dokar a kamfaninmu, yana da muhimmanci da farko ka shawarci mutumin (mutanen) da kake tunani suna yin abinda bai dace ba. Taimaka ka shaida mana idan kai kanka ka taba cin karo da keta dokokin da'ar aiki.

Bisa ga yanayin keta dokar, za ka iya kai rahoton abin da ya faru zuwa ga manajanka ko mai lura da aiwatar da bin doka Annelie Gröniger:
compliance@dw.com
+49.228.429-2105

Haƙiƙa, za ka iya tuntuɓar mutanen da suka dace, musamman wakilin ma'ikata ko, idan ya zama tilas, jami'i na waje mai lura da cin hanci ko ka tuntuɓi mutanen da ke da alhakin kula da kariya ta tsangwama dangane da jinsi.

Ko a wane hali, tabbas hakika za a ɗauki rahotonka da matukar sirri.

## Matakan da DW za ta ɗauka idan aka sami keta doka

Idan aka karya dokoki, DW za ta ɗauki matakan da suka dace domin fayyacewa. Wadannan matakai za su kunshi tattaunawa da ma'aikacin da abin ya shafa domin baiyana masa muhimmancin kundin da'ar aiki da manufar kawo sauyi ga halayyar wannan mutum ta la'akari da dokokin da ke kunshe a kundin da'ar aiki. Yana iya yiwuwa laifin da aka aikata ya kai ga daukar wasu matakai a cikin tsarin dokokin da suka dace da kuma dokokin ƙwadago.